## Addu'a da furuci game da neman nun iko

*Uba, ina yi maka godiya domin kai ne ka harhadani a cikin cikin uwa ta. Ina godiya domin kana kauna ta, ka kuma kira ni naka. Na gode domin zarafin da na samu in zama mai bin Yesu Kristi.*

*Idan ka yarda, ka gafarta mani marmarin da nake da shi na nuna wa wadansu fifiko. Ina ki, ina kuma yin watsi da wannan irin marmarin. Na ki in yi farin ciki da tunannin cewa na fi wadansu. Na yarda cewa ni mai zunubi ne kamar kowa, kuma ba zan iya tsinana kome ba idan ba tare da kai ba.*

*Na tuba, na kuma ki daukar da nake yi ta cewa kungiyarmu, kabilarmu, ko jinsinmu shine yafi fifiko a cikin jama'a. Na yarda cewa dukan jama'a daya suke a gaban ka.*

*Na tuba da kalmomin kaskanci da na kiyayyar da na ambata game da wadansu, ina kuma rokon ka gafarta mani wadannan kalmomin.*

*Ina kin daukar mutane a bakin ba kome ba sabili da harshensu, jinsin su, dukiya ko iliminsu.*

*Na shaida cewa alherin Allah ne kadai ya bani damar tsayawa a gabanka. Ina raba kaina daga kowace irin shara'antawa ta mutane, ina kuma duban ka kai kadai domin samun ceto.*

*Ina raba kaina da koyaswar Musulunci wadda ke nuna cewa masu adalci sune suka fi fifiko, cewar Musulunci yana sa mutane su zama masu nasara, da kuma cewar Musulmi suna da fifiko a bisan wadanda ba Musulmi ba.*

*Na ki, na kuma yi watsi da ikirarin nan dake cewa maza suna da fifiko a bisan mata*

*Uba na sama, ina juya baya ga dukan daukaka ta karya, a maimakon haka, na zabi in bauta maka.*

*Ubangiji, na kuma zabi in yi murna yayinda wadansu suke samun ci gaba. Ina ki, ina kuma yin watsi da dukan kishin wadansu.*

*Ubangiji, ka bani hikimar sanin matsayina a cikinka. Ka koya mani gaskiyar yadda kake gani na. ka taimakeni in zama da gamsuwar matsayi da kuma yadda ka yi ni.*